Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Glorious (Majidu)." https://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/infiraji-1-majidu/.

# Majidu

[Cover page]

Waƙar Infiraji Ta Farko

Waƙar Majidu

Al-Nāshiru Aḥmad al-Tijānī, Ḥafiẓahu l-Lāhu

Waffaqahu Allāhu ilā mā yuhibbu, āmīn!

Bi idhni Mu'allifu hādha l-kitāb

Alhaji Malam Aliyu Namangi

Zaria

[End Cover]

Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Glorious (Majidu)." https://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/infiraji-1-majidu/.

[Page 1]

Bismi l-Lāh al-Raḥmān al-Raḥīm. Wa ṣalla l-Lāhu ʿalā l-Nabiyyi l-Karīmi

Wa ʿalā ālihī wa ṣaḥbih wa sallam

Bismil l-Lāhi Majīdi — Na yi nufin waƙa jadīdī

In yabon manzo ḥamīdī — Dhu shafā Yawmal Miʿādi

Mai sonsa ba zai baƙin ciki ba

Rabbanā ya daɗin aminci — Gun mafificin mutunci

Ɗa wani nasa ɗan karumci — Wanda ka ba shugabanci

Ya yi horo ba da kangara ba

Gaisuwata ko ta dace — Gun ma'aikinnan da'ance

Ran Musulmi kar shi sance — Bisa sonsa mu kau amince

Mai sonsa ba zai baƙin ciki ba

Rabbi na nufi wagga waƙa — Ta yabo nasa ba nifāqā

Taimake ni ka ban ḥadhāqā — In yi waƙa mai zalāqā

Ta yabo nasa ba da kuskure ba

[Page 2]

Rabbanā ka yi min ijābā — In ga nai sallah a Ɗaiba

Har in tada ido in duba — In ga Koran nan ta gubba

In yi murna ba da fariya ba

Ya Ilāha l-ʿālamina — Taimakan ni in je Madina

In ji daɗi in yi murna — In ga qabrin ɗan Amina

Baban Kulthumu ɗan Suwaiba

A dare ka yi min ishārā In ga na je nai ziyara

Gun kushewan na da nura Ta cika shi na mai bushara

Ga Musulmi ba da kangara ba

Ka ji mai waƙar hululu Tūba zanka yabon Rasulu

Musɗafa jikankKhalīlu Gobe ka sha salsabīlu

Wanda ya fi ruwan zuma a gumba

Don mutum ne shi karimi Mai yawan haƙuri ḥalīmi

Ya abokina ʿAsīmi In ka so ka zame salami

Ya bi Annabi ba da sunkuye ba

[Page 3]

Kafirai da sun fahimta Bin Muhammadu ya kamata

Ambato nasa ya gabata Can ga Attaura, ku huta

Ku bi Annabi ba da gardama ba

Ya kamata mu gode Allah Can gabanmu akwai qabīla

An kashe su cikin jahālā Mu zuwansa tazan fitilla

A gare mu ba mu yi zaman duhu ba

Shekarar ƙarnin dashensa Ya katarta da maʾu nisa

Shi muke cin arzikinsa Ka ga ba don shi ba da sa-

Muwa ba ta riski mai rashi ba

A'a in ba ka mayyaze ba Gaskiya ba ta sa fita ba

Sai da ya zaka nuna turba Ko duhu bai wartsake ba

Ba dan aiko shi duniya ba

Ɗan Amina muna yabonka Don mafificin rabonka

Nai duʿāʾi in gane ka Zuciyata ba ta harka

In ban yi yabonka na natsa ba

[Page 4]

Sanda an aiko shi shirya Gaskiya ta kori ƙarya

Masu aikin ratse hanya Ƙi da so wasu sun biyayya

Tamkar ba su gaji kangara ba

Shi mutum ne mai laɗafa Kyan jiki da hali da siffa

Na ga Annabi ba khilāfā Ko a baiwa ya fi sarfa

Ba shi kan kyauta shina bari ba

Ba shi rowa don ƙiyayya An yi sammu gami da cinya

Aka ba shi a kan hamayya Don yawan ladabi da kunya

Ya ci ba bisa kan rashin sani ba

Hankalinsa yana ga Allah Bai kula ba, maras kasala

Gun yawan azumi da salla Taimakonsa yana ga Allah

Ya ko isa jalla bai gaza ba

Rabbanā ya baza wanjin Masu ƙinsa sabo da ƙwanjin

Arzikinsa ya haske ƙirjin Annabinsa aboka bar jin

Maganarsu ba su yi muwāfaqā ba

[Page 5]

Shi ya ɗaukaka ɓirbishinsu Hassadarsu ta hallaka su

Aka karkashe galibinsu Galibin wasu masu mussu

Suka tuba da sake ba shi gaba

Rabbanā ya keɓe bawa Nai mafificin muruwa

Kamili a barin adawa | Zuciya ta sa ba ta gawa

Ba shi kan ƙi mutum akan rashi ba

Shi tawāḍiʿu ne halinsa | In ya hangi mutum a nesa

Sai ya tashi ya je su gaisa | Don cikakken hankalinsa

Dubanshi da kai ba shi yawa ba

Ban hannu don girmamawa | Nasa ne ke kwaikwayawa

Kwarjini mai tsoratarwa | Na ga Annabi ga ʿulluwa

Amman ba shi kan takabbura ba

Don adalci shi uwa ne | Gun marayu kau uba ne

Ko da ya zama shugaba ne | Ba shi ce maka ya fi wane

Tun bai haɗa shekara bakwai ba

[Page 6]

Mai ado da yawan ḥuḍūri | Ga sifa marashin quṣūri

Shi mutum ne Dhā waqāri | Lazimin istighfāri

Ba tare da ya yi laifuka ba

Wa ya kai wa yai kamarka | Wa ya san asali ya naka

Wa ya san matuƙar rabonka | Tun da Allah ya yabe ka

Duka wanda ya ƙi ka ma yi gaba

Rabbanā ya girmama ka | Tarsashin sauran ma'aika

Kowane na ƙarƙashinka | Jalla yai baiwa gare ka

Wacce bai yiwa duk ba annabe ba

Duk maso rahama ya bi shi | Tutture ma ya yi nishi

Ya yi kewar kar ya bar shi — Sannu mai lugude da mashi

Ga waɗanda ba sui muwafaƙa ba

Ɗan uwa bawan mushi'a — So shi domin kyan ɗabi'a

Binsa bin hakkin sharia — In yabonsa ya zam sana'a

Ka, ba ka tozarta lahira ba

[Page 7]

Ni yabonsa naka lazimta — Ya ishe ni biyan bukata

Duniya har ma mu huta — Ran da tsayuwa ta tsananta

Ka aje mu a dama ɗan Suwaiba

Sannu mai huska da haiba — Ambatonka da shi na saba

Ya ishe ni tsarin musiba — Wanda bai so Musɗafa ba

Ba zai daraja a lahira ba

Shi mutum ne mai hanana — Gun Musulmi ba khiyāna

Zuciya ta sa ga i'āna — Ga kiyayewar amana

Shi bai taɓa saɓa alkawar ba

Shi mutum ne ɗan halali — Gun uwa da uba ga hali

Gun tsayawa kau jamīli — Wāsiɗi ne ba Ɗawīli

Ba wada ne maras tsayi ba

Ya fi kowa fai da ɓoye — Aiko shi duhu ya yaye

Zuciyar kowa ta waye — Ga sifa mai bada ƙaye

Ga kyauta ba da kwarmato ba

[Page 8]

Ga yawan natsuwa da iffā — Ga shi kyakkyawa ga siffa

Ga kiyayewar haruffa In shina batu ba khilāfā

Harshensa baya gura-gura ba

Madugun Makka dakace ni Za ni kewa ta ishe ni

Ɗaiba gun kakan Husaini In yabo a cikin sukuni

A gaba nasa ba da shamaki ba

Ya maji roƙon gazajje Rabbana tashe ni in je

Ɗaiba in ga mafi mazaje Kwarjini ga kyau da saje

Da wushirya ba ta famfara ba

In gabata da gaisuwata Gun mafificin halitta

In faɗa masa ƴar-bukata Ke gareni da ta tsananta

Dan bai taɓa ƙyalle mai-kira ba

Sannu zaɓaɓɓen ma'aika Arziƙina ambatonka

Zuciyata na yabonka Hankalina na gareka

Tun gaban ba mu taru jin kira ba

[Page 9]

Ya matsera ya madafa Ya mafi tausan mahaifa

Ya matsamar wanda ya fa -ɗa zurfi ba mu ƙofa

Da take hannunka ba rufewa

Ya mafificin fiyayyu Ya mafi rainon marayu

Ƴan kanana har sushiryu Rungumemu kace Aliyu

In munka rabo baka rasa ba

Ganuwarka da ba ta riɓɗa- Gun Muhammadu, nan naraɓa

Ya mafi adu'a a karɓa Tun da kai Allah ya zaɓa

Komai kafaɗa ba'a musa ba

Ga mu gun jikanka Shehu — Don isar kakanka Nuhu

Rungume muka ce madihu — Wanda ke da uwa a murhu

Ba zai ci tuwonsa ba miya ba

Ya kamata mu gode wanda — Munka san kalmar shahada

Arzikinsa farin jakada — Wanda ke da isa a fada

Jama'arsa ba su yi baƙin ciki ba

[Page 10]

Ƴan uwa mu yawaita murna — Zuciyarmu ta daina ƙuna

Annabimmu ya zo da sunna — Duniya haske ya zauna

Har gobe ba'ai zaman duhu ba

Ɗan Amina mafi daraja — Ɗa waninsa, mijin Hadija

Rabbanā ya ba ka hujja — Wadda ba ta ga mai darajja

Wani in ba kai ba Ɗan Suwaiba

Rabbanā ya kira ka ka je — Inda ba wani wanda ya je

Ko a zuci cikin mazaje — Kai da takalmanka ka je

Ka ga Allah ba da shamaki ba

Shi ya ce maka Marhaban ya — Masoyi wanda shiriya

Na gare shi, kusanta gaya — Mai jidali dubi aya

Ka ga kalma ba ta gardama ba

Ya kusanci gadon sarauta — Jin kiransa shina yawaita

Arzikinsa shina tsawaita — Anka ce Ƙaro kusanta

Magana ce ba a bar musu ba

[Page 11]

Anka ce da muqarrabuna Ku yi ciri ga Annabina

Nai kiransa bisa amana Anka ce ka shigo ka zauna

Da ka je ba ka dafa shimfiɗa ba

Sai da kai tahiya ga Allah Anka ce lale fitilla

Mai kawar da duhun jahala Mun kira ka mu ba ka salla

Ya ji kalma ba ta ɗan adam ba

Sai da yai sujada da goshi Nai ga wanda ya ɗaukake shi

Anka ce ya cira ya tashi Ya katarta ga wanda yai shi

Ba a mai matuƙa ga ɗaukaka ba

Anka ba shi dukkan ibada Don shi kai mana mui ifāda

Wanda yai tsauri ya kauda Kansa ya taɓe, da wanda

Bai girmama wanga Annabi ba

Mai jidali daina mussu Annabawa tarsashinsu

Musɗafa ne Shugabansu Ko da ya zaka ƙarashensu

Darajarsu da shi ba'a gwada ba

[Page 12]

Kowane aka ba shi aiki Sai a mai adadi da yanki

Inda za shi kira da mulki Shi da kau aka ba shi aiki

Ba a mai adadin abin kira ba

Arzikinmu ya tsaga dutse Tun da zaɓaɓɓe nitsattse

Wanda ke tsamo nitsattse Ya riƙe mu da so, ka rantse

Ran gobe ba mui baƙin ciki ba

| | |
|---|---|
| Kyan ɗabi'a na gare shi | Wanda in ka ji sai ka so shi |
| Ba shi baiwa don a ba shi | Ba shi alkawari ya tashi |

Don ba halinsa yaudara ba

| | |
|---|---|
| Ba shi zobe in ya ba ka | Ba shi jin ƙyashin abinka |
| Ba shi son mai tseguminka | Ba shi zargin mai yabonka |

Don ba halinsa hassada ba

| | |
|---|---|
| Ba shi ƙyamar mai talauci | Don rashi ba ya butulci |
| Ba shi ƙin kallon halacci | Ba shi kau kallon haramci |

Tun ba makaɗa da ƴan dabo ba

[Page 13]

| | |
|---|---|
| Sannu Ɗa mai kyan tsayawa | Mai yawan fara'a da baiwa |
| Ce da ni, ranar tsayawa | Tarsashin zunubanta nawa |

Ba za su hana mu saduwa ba

| | |
|---|---|
| Sannu mai huska sakakke | Wanda ya fi wata ga haske |
| Sannu mai siffa cikakke | Maganinka na sha na warke |

Domin iliminmu bai yawa ba

| | |
|---|---|
| Rabbanā domin Muhamman | Don Sahabbainai ʿumūman |
| Na baraci zama a laiman | Shugaban bayi Muhamman |

Jikan Adnana ɗan Suwaiba

| | |
|---|---|
| Yā Ilāha -lʿālamīna | Taimaka ni in je Madina, |
| Gun Muhammadu Ɗan Amina | Rabbi ranmu shi huce ƙuna, |

A gaban ajalinmu bai kira ba.

Wanga talifi da na yi Waƙe-waƙen masu caji

Nai ma ƴa ta ce Ajuji Sai nasa mata Infiraji

Mai yinta ba zai baƙin ciki ba.

[Page 14]

Yau fa waƙa ta taƙaita Kulluha sittūna Baytan

Sai takwas bayan cikinta Ɗan Ashin Hijira mu kaita

Ta ko cika ba da gardama ba

Alḥamdu li l-Lāhi Rabbi l-ʿālamīn.

Tammat bi ḥamdi l-Lāhi

Wa l-ṣalātu wa l-ṣalāmu

ʿalā l-Rasūli l-Lāh

Bi qalami Ibrahim

Yaqubu Gusau